[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: ?*ARNAN DAJI*?

FAREEDA ABDULLAHI

*BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DASUNAN ALLAH ME RAHMA ME JINKAI INAFATAN ALLAH YA TEMAKENI YABANI IKON RUBUTA WANNAN LABARI DANA DAKKO BA AKAN WANI KO WATABA KAGAGGEN LABARINE WANNAN SHINE LABARINA NA FARKO INAFATAN ALLAH UBANGIJI YABANI IKON YINSA CIKIN AMINCI KUBIYONI DAN KUGA IRIN SALON DAYAZO DASHI*

NASADAUKAR DA WANNAN LITTAFIN GA MAHAIFIYATA WADDA TA RAINENI TA KULA DANI TSAWON SHEKARU MASU YAWA JINJINA GAREKI MAHAIFIYATA

1-5

Garin kuguru dajine wanda wasu mutane ke rayuwa a cikinsa basu dawani addini dayawuce bautar wani katon gunki Wanda duk shekara sai anyanka masa mutane guda biyar yasha jini sukuma mutan garin suci naman suna bikinsu na al'ada duk shekara suna fita iyakar garinsu suna kama mutane duk Wanda Allah yasa tsautsayi yashigo dashi dajin suna kamasu su dauresu sai karshen shekara suyankasu subawa gunkinsu jinin sugasa naman aci asha burkutu basu da wata sittira sai dai susa fata ko ganyaye su rufe gabansu da ita matan Kuma su dan kara a mamansu idansun zama yammata suna daura auren duk wata budurwa a karshen shekara a abikinsu na shekara shiyasa ba karamin gagarimin taro akeba sarkin garin azzalimine bashida imani ko kadan idan kuma kikai haihuwar fari za a dafa dan acinyeshi Wanda sai anfara kaiwa sarki naman wannan kenan.

Tenkwai tenkwai way kina inane kije kidebo mana ruwa a rafi kinsan gidan nan bamu da ruwa ko kadanko ko sai dare yayi kinsan garin nan almuru na kawo Kai ba a zuwa rafi saboda

mugayen abubuwan dake hanyar,Kai lamunde ganinan bara nabiyawasu rama, da aduke,sai mutafi yauwa kuyi sauri dai karku jima,tenkwai tasa kai da tulunta a hannu tana tafe tana wasa tabiyawa rama da aduke suna tafe suna hirar wasan daza ay na wannan shekarar aduke tace tenkwai wayko meyasa haryau kinki kisaurari ja'ene yakamata izuwa yanzu kibashi hadin kai tunda kinga har yanzu baki Sami Wanda ya kwanta mikiba tenkwai ta kalleta tace nifa banasan wannan rayuwar ta mutanen garinmu kawai Dan bansan yadda zanyiba amma gaskiya wannan yanka mutanen banasansa duk fa jinsunmu daya irinmu guda kuna kallo idan aka rasa mazanmu ake yankawa kanaji kanagani za a yanka abunda kahaifa Dan rashin imani ba afita agarin nan bame shigo mana duk wanda ya shigo sunansa matacce inafatan sanji yazo mana a wannan gari nisam bansan ja'e saboda dan sarkin garinnan ne shima bashi da imani tamkar mahaifinsa kinsan Kuma insarki ya fadi shine sarki  amma zankara tunani akai zanyi shawara da lamunde.

Anan suka nemi waje suka zauna sunata hiarsu da hirar yanda wasansu na  wannan shekarar zekaya yarda ake wasa da wuta awajen da macizai  aduke tasa tulunta tana debo ruwa tanata basu labarin saurayinta tace tana dagowa saitaga kamar wani abu na yawo asaman ruwa tazabura ta firgice ta kwalawa  tenkwai wani razanannen Kira dubamun kamar abu nake gani asaman ruwannan menene wannan tenkwai jaruma batada tsoro zuciyarta adake take amma akwaita da tausayi ta matsa kusa rama da aduke sai ja da baya suke tasa kafarta tashiga ruwan tana jawowa saitaga wani abu tasaki wata razananniyar kara wadda ta furgitasu gaba dayansu suka zura da gudu sukabarta a wajan tana maida wani irin numfashi saboda bata taba ganin irinsaba tunda take a rayuwarta.

Shin me tenkwai taganine daya furgitata kubiyoni a page nagaba.

*Feedyn bash*

[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: ?ARNAN DAJI?*

*?KAINUWA WRITERS?? ASSOCIATION??*

{United we stand and succed;our ambition is to entertain &motivate the mind of readers}

FAREEDA ABDULLAHI

10-15

NASADAUKAR DA WANNAN PAGE DIN GA MASOYA WANNA BOOK NAWA INAJIN DADIN YADDA BOOK DINA YA KARBU GAREKU JINJINA AGAREKU MASOYA ????????????

A guje lamunde ta karasa kanta kafin ta isa micijin ya gudu tarasa yadda zatay ga tenkwai a kasa a kwance ga wani mutum daya firgitata ta rasa yadda zatay tadinga zagaye chan ta tuna tajanye mutumin zuwa wani surkukin chan cikin dajin tausayinsa ya ratsata ta dawo kan tenkwai taruke ta idonta yasanja kala yay kore shar aguje ta direta tabazama dawa akwai wani masanin micizai cikin dajin shiyasan kan dajin tana zuwa ta zube ta rushemasa da kuka durka katemakamun diyata na tsakiyar daji maciji ya sareta katemakamun a firgice ya Mike ya dakko jakar maganinsa ta fata ya biyo bayansa suna zuwa yana kallonta yace wannan kububuwace waddata addabi mutannen Bata taba saran wani be mutuba itama wannnan diya taki ba saranta tayiba hucintane amma yanzu zan mata magani ya dukufa nan da nan cikin sa a tadawo hayyacinta lamunde tadinga zabga masa godiya ya tashi ya koma dawa jiki b kwari yana ina lamunde yana ina kitemakamun munemoshi mutemakeshi banaso suganshi sukamashi lamunde ta toshe mata baki nina noyeshi Dan kar me magani yaganshi tashi muje mu dakko shi takamata suka mike da kyar take tsaiwa amma haka ta karfafi jikinta suka nitsa dawa lamunde ta dagashi dakyar tenkwai ta temaka mata suka fara tafiya saboda gari harya fara haske

Ana idar da sallah ta kwalawa me aikinta Kira ke maryama zonan aguje tafito saboda masifar tsoronta datake zan fita asra da ansar basu tashi ba idansun tashi ki kula dasu ki hada musu abinci ki shiryasu su tafi makaranta ni natafi tasa Kai tabar gidan oh ko ina zata da duku duku haka Allah ya kyauta ita mijinta ya Bata amma ko ajikinta wani farin cikima takeyi tasa Kai

ta koma dakinta a guje take tukin kamar zata tashi Sama tana zuwa kofar gidansu afra tadinga danna mata horn  takirata kefa nake jira gani nan jarababbiya uwar rashin hakuri fitowa zanyi tana fitowa ta shiga gaban motar kawata baki da hakuri da rayuwa duk wannan abun da kikai be ishekiba sai kin hada da boka yazama dole kodan muci kudi hankalinmu kwance amma da suhail ya tara kudi iya kudi yahanamu mu wala bayasan yabarni naje wasu kasashen shi kawai sai wata saudia nagaji da zuwa sai Egypt itama sai dai banda lafiya suko yara kina kallo sai dai akaisu jidda inaso inzama big madam yaki yanzu ay kinga yaywa kansa yana barzahu mukuma muci kudi mi wadaka muje kasar damukeso mu wataya hhhhhhh suka kyalkyale da dariya kina wutaaa wallahi inabinki da gas chewar afra sai wajen goma suka shiga garin zariya saboda sun hadu da cinkoso a hanya nan suka dauke hanyar makarfi suka nutsa cikin wani daji suka tsaya inda mota take tsayawa nan suka fara tafiyar kafa suna hawa dutsuna suna sauka saida sukai tafiyar awa guda sannan sukazo bakin wata katuwar tsamiya nan sukaji wani amo mara dadin saurara nan aka kyalkyale dawata mahaukaciyar dariya muguwa Yar gidan muguwa kinyo gado gado ba karambaniba naga komeke tafe dake abu guda dayane tsofaffinnan bazasu manta da dansuba bazasu dena masa addu a ba abu daya za'ay zamu cire musu tunaninki aransu bazasu kara zuwa wajenkiba bazasu karayi miki maganarsuba Amma sai kin maida musu da yayansa shi kuma kaninki angama dashi ga wannan kije tsakar rana karfe daya kidinga turare kina ambatar sunansu tsawon kwana uku to boka ga wannan a asiyawa aljanu shanu su sha jini ta ajiye bandir din yan dubu dubu guda goma hhhhhhh kufita da rarrafe aka daka musu tsawa da rarrafe suka taho suna tahowa sunzo dai dai wani dutse suka hada ido da ita suka zubaa mata ido cikin tsananin mamaki a matukar razane ta kallesu.

(Anan zan dakata fans sainaji ra ayoyinku yawan comment dinku shike kara mun karfin gwiywa cigaba da rubuta wannan littafin nice taku a Koda yaushe )

*Feedyn bash*
[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: ?ARNAN DAJI?*

*?KAINUWA WRITERS?? ASSOCIATION??*

(United we stand and succed;our ambition is to entertain &motivate the mind of readers)

FAREEDA ABDULLAHI

5-10

Cikin firgici ta kara kallonsa taganshi kwance lankwam cikin ruwa Bata taba ganin mutum me kyau irinsaba tabbas wannan badan yankinsu bane ruwane ya kodashi nan gabar to amma kamar fa be mutuba tasa iya karfinta tajawoshi saitaga kansa a fashe yanata zubar da jini tasa kunnenta akan kirjinsa taji yana numfashi ta jawoshi gefe taboyeshi abayan bishiya yadda ba wanda zeganshi ta shiga daji tadebo ganyayyaki na tsaida jini tasa a wajen dayay rami ta dinga danna cikinsa ruwa yanata fitowa ta hanci ta baki amma be farfadoba yanata dai attishawa,

Da gudu aduke tashiga gidan tana Kiran lamunde yau mushiga tara badu ya temakemu tenkwai tana bakin ruwa tayi gamo lamunde ta dora hannu ta dinga runtuma ihu Kira take badu katemakeni ka kubutarmun da yata ita kadaice dani banda kowa banda komi sai ita kadai badu ka kawon temako rama kuwa tuni tagarzaya gidan sarki tana zuwa abakin shiga tagamu da ja e tazube tana haki fadi take jinjina gareka magajin kaho badu ya temakeka tenkwai na bakin ruwa tayi gamo inaga zuwa yanzu ba tenkwai kaimun aikin gafara sarkin gobe yana jin wannan magana ya mike a zabure ya saki wani ashar nan da nan ya kira fadawa suka dunguma sai daji suna bakin ruwa suna tafe sunata zage zage.

Tana zaune ta dora kansa akan cinyarta tajiyo kamar hayaniya daga chan nesa da sauri ta tashi tajashi chan chiki wajen wata bishiya tayi nesa da bakin ruwan tay maza tadawo bakin ruwa tana fitowa suka karaso ja'e ya kalleta ta kalleshi yace inayake meyasameki a gigice yake tambayarta tace ba komai naga jini a jikinki meyasamekine me kike boyemun bakomai nagayama wani dabbace tafito daga ruwa Amma na kasheta ba abunda yasameni kintabbbata tace hakane yadakawa fadawan wata mahaukaciyar tsawa yace Kai kuduba lungu da sako kuga bawani abu nacutarwa anan nanda Nan suka bazu cikin dajin da gefen koshin suna lalube hankalinta yay masifar tashi dataga daya ya durfafi wajen data boye shi tadinga addu ar badu yatemaketa har ya kusa zuwa wajen ja'e yakwalo masa Kira yace kai kuzo mutay ku dakko wayan nan tulunan dukansu yasata agaba sai wayensa take suna tafe ja'e yanata mata hira

Amma Sam hankalinta baya kansa yace ki amince dani bikin shekarar bana tunda yakusa a daura mana aure mutum daya ake nema daga nan zuwa wata biyu masu zuwa za agabatar da bikin ki amince dani ina Sam Bata San meyake cewaba hankalinta yana kan wannan mutum data tsinta abakin ruwa tana fatan karya farka ya shigo gari akamashi tunda dama mutum daya ake nema hankalinta yatashi gashi ba a shiga wannan dajin da daddare yanzu yazatay meye mafita sai da ya tabota sannan rayi firgigit Koda wata matsalane a a ko tunanin aurenmu kike tay yake yace karki daga hankalinki duk wata wahala ni zan dauke miki ita baku da matsala tace kabari zanyi magana da lamunde yadda mukayi zangayama ya bata rai ita zata zauna dani toko kinasona ko bakyaso kishirya aure a wannan shekarar nagaji da binki danake kina mun wasa kinsanni kinsan halina nine magajin garin nan Dan haka dole na samu abunda nakeso ban taba nema abu na rasaba bazan Fara akankiba nagaya miki dankinga inasanki a fusace ta juyo ta kalleshi tsakar ido saboda bata da tsoro tace bance bazan aurekaba amma baka isa kaimun dole ba sai nayi shawara Dan ba a karkashin kanakeba balle kaimun zalincinka daka saba ransa a matukar bace yace ni kike gayawa haka ya daga hannu ze mareta tarike hannun tace karka Fara Danni ba sakarya bace tawuce tabarshi rai bace.

Laminde na zaune kawai taga tankwai ta shigo kamar anjehota tana huci da gudu lamunde taringumeta tana kuka tace akacemun wani abu ya kamaki a bakin ruwa ki kwantar da hankalinki ba abunda yasameni ina cikin kwanciyar hankalina duk inda nake badu yana tare dani kawai tsorone irin nasu aduke tace nifa nagafa abun asaman ruwa amma kice ba komai dagaske nake gaya miki banga komai ba kawai wata dabbace a ruwa kuma na kasheta ku kwantar da hankalinku ga shi chan ankai muku tulunanku gida maza kuje kar anemeku nagode maku.

Way lafiyarki tunda kika dawo kin kasa magana ki zubawa waje guda idanu ko dai kinyi gamone tenkwai dakefa nake magana lafiyarki kuwa ta girgizata sannan ta dawo hayyacinta laminde ke babatace bazan iya boye mikiba na tsinci wani mutum a cikin ruwa na boyeshi a cikin daji banasan wani abu yasameshi saboda ba irinmu bane ba dan nan garin bane idansuka ganshi zasu kasheshi yabani tausayi kitashi mu shiga daji mu dakko shi heyyy tenkwai meyake damunkine kinfi kowa sanin gagarimar matsalar dake cikin dajin shin way ma waye shine kinsan idan aka kamamu munshiga tara wajen sarki kaho kawai kibarshi har y tashi achan tunda kintemakeshi ya koma inda yafito ta cikin ruwa tun kafin yan gari su farga dashi su cimmasa lamunde haka baze yiwuba inajin tausayinsa Dole muje mutemakeshi to kobari da duku duku kafin gari ya idda wayewa sai mu tay muzo dashi Amma inajin tsoro sosai karki damu lamunde ba abinda zefaru inajin hakan a jikina cewar tenkwai.

Momy momy ina daddy na yau kwana biyar banganshiga kince zedawo daddy beta Mana haka ba ko baya kasar nan yana kirana Kuma har yanzu kince ze dawo wallahi asra zanci ubanki yana chan yayi tafiyarsa yawon iskancinsa zaki dameni matsa kiban waje karna hambareki asra tasa kuka takama hannun ansar kaninta suka shige dakinsu sunata kuka da begen daddynsu kai tsaye ya sawo kai cikin falon yana wani mugun wari na Yan maye cike da maye ya kalleta komai ya kammala kimanin kwana biyar mun batar dashi daga doron kasa mu kasheshi mun cilla gawarsa cikin ruwa hhhhhh ya sheke d wata mahaukaciyar dariya dan haka kibamu rabonmu nida abokaina a wulakance ta kalleshi kai yahuza nifa yayarkace baka da mutunci wlh Dan kunmun wannan Dan karamin aikin sai na biyaku a wajenku wannan ba komai bane Kuma kasan idan wayannan tsinannun iyayen nasa sukaga nafara wadaka da kudi zasu dago wani abu kanagani sun kasa tsaye sun kasa zaune neman mafita kawai suke naji labarin angano motarsa a bakin titi inda kuka daukeshi dazu al ameen kaninsa yazo yake gayan shima zasu tsananta binkice akansa sunata addu a kasansu kabari ba yanzuba sai komai ya lafa sun hakura ke kin isa cewar yahuza wallahi Jeddah kinyi kadan koki bani ko yanzu ki bishi inda yaje ba mijinki bane ba dukiyarku bace dallah malama bani ko yanzu na farke miki ciki kiga Yan hanjinki a waje na dibi abinda zan diba Jeddah jiki na rawa tace baya ajiye kudi a gida kasani kudin gidan duka bazasufi dala dari biyu b to wallahi sai dai ki hadon da sarkokin ki masiyar shegiya me rowar tsiya uwarkima ba Bata kike ba duk da itama shegiyar ita take daure Mana gindi (wa iyazubillah fans kunji fa uwa dakanta Allah Kai mana kyakykyawan karshe kabamu iyaye nagari) bare mu kannenki ke kanki kin mallaki dukiya me tarin yawa saboda mijinki ya sakar miki komai Amma saboda San  zuciya irin naku keda uwarki duk da mora mata kikeba kuka yanke masa wannan hukuncin kuma Ni kinsan dole a biyamu wlh tashi ki dakkon kudi yadaka mata tsawa da gudu tashiga daki ta hado duka sarkokinta ta dakko masa duka kudin dabatasan adadinsuba Amma daloline Dan tasan halin yahuza bashi da imani kanintane cikinsu daya amma besan wani abu way shi tausayi ba tana kawo masa ya sheke da dariya yace shegiyar kaya ganin kabari mesa a tuna Allah ya warce ya kara gaba yana fadin zan dawo Dan ba wannan ne kawai kasonaba yana fita talalubo wayarta ta dakowa kawarta Kira tana dagawa tace afra kina ina maza maza kizo muje wajen boka akwai matsala wannan shegen yaron yahuza zeban matsala da wayannan dattijawan iyayyen na suhail wallahi basu isaba  maza kizo haba Jeddah la'asar fa tayi koso kike sai dare zamu isa kiyi hakuri zuwa asuba sai kibiyo kidaukeni kinsan hanyar Bata da kyau shikenan amma Dan Allah ki shirya da wuri bamatsala sai goben nagode

Tenkwai kwance tana ta juyi takasa bacci kawai hoton wannan mutumin take gani tunda take Bata taba ganin mutum me kyansaba ya burgeta yanada kyau me daukan hankali ita tunda take Bata taba ganin mutum me kyansaba wacece tenkwai yace awajen lamunde da aska mahaifinta ya rasu tun tana shekara tara ita kadaice wajensu lamunde ba wata kyakykyawa bace ta tashin hankali tanada dai kyanta dai dai nata sai dai fa akwai dukiyar fulani ga maka makan maxaunai ga hips Kai abundai ba a magana idan tana tafiya Dole ka shagala da kallonta saboda takuntama abun kallone tana taku day sai jikinta yay wata girgiza me tadawa maza hankali kaf garin kuguru ba wata matashiya budurwa me diri irin nata sai dai afita kyan fuska gata da kyan hali uwa uba nutsuwa da tarbiyya kamar ba mutuniyar daji ba tana da tarin masoya saboda Allah yay mata farin jinin samari duk cikinsu b wanda take kulawa sai gashi Dan sarki kaho ja e yana nemanta shiyasa kowa ya janye sabod masifar tsoronsu da akeji a gari bashi da imani ze iya sawa a fillema Kai baruwansa tayi juyi takasa bacci kawai burinta gari ya waye lamunde tayi juyi takalleta tace ki kwantar da hankalinki zan temakeki ki dakko shi kikawoshi nan har ya warke sai mu sashi a hanya ya hanzarta barin garin nan indai kinyarda da murna da farin ciki nayarda lamunde shiyasa nake kara kaunarki banda kowa saike a garin nan karki damu Amma ki samu wadataccen bacci.

Ja e nashiga gida rai a matukar bace ya shiga dakin mahaifiyarsa yana huci asalin mahaifiyarsa fulanine irin masu yawo hanya ta kawosu kusa da garin kuguru tsautsayi yasa sarki yazo giftawa ya gansu yasa aka kamesu agabanta ranar bikin shekara aka yanka babanta ya aureta a ranar mahaifiyarta ta hadiyi zuciya ta mutu bakin ciki yay mata yawa tadauki alwashin saita kawo karshen wannan zalunci tayaya Bata da me tallafa mata kyakykyawace ta karshe   itace matar sarki kaho ta 34 duk cikinsu ba wadda ta taba haihuwa dashi ko batan wata haka tanaji tana gani tazama matar kaho wata su uku da aure ciki ya billo bakin ciki wajen sauran matan ba a magana gashi sunsan halin sarki kaho akan cikin ze iya sawa a fille musu kai ahaka a tsa gwame ta haifi ja e suka hada kansu suka tura amintacciyar baiwarsu guda wajen boka sukasa yay mata abunda ba ita ba kara haihuwa yace angama yabasu magani sukasa mata a kofar dakinta tunda ta tsallaka shikenan itama Bata kara haihuwaba bayan ita ya auro mata goma sha biyu suna Nan Amma ba wadda ta kara haihuwa a gidan shiyasa ya dau San duniya ya dorawa ja e duk wannan yanka jaririn farko da ake ba ayanka ja e ba saboda dan sarki ne Kuma ba wanda ya isa yay magana akwai Wanda yay magana a fada a take aka yankashi akay farfesunsa sarki yace shine madadin ja e tsabar zalunci ja e sunan mahaifin hure ne mahaifiyarsa shiyasa take sansa Bata da yadda zatay gaskiya hure dole a dauran aure da tenkwai wai harni zatacewa bazata aura ba setayi shawara wacece ita to zanje zanyi abunda nakeso kamar yadda nasaba da duk wadda taymun Dan dai kawai inasanta shiyasa nace zan aureta Amma Ni zata dinga gayawa magana mata nawa gareni inada mata ashirin da biyar hure

ta gyada Kai tana me alla wadai da wannan rayuwa dasuke ciki tace kar Kai haka ka kwantar da hankalinka zanje har gida nasameta zaka aureta cikin bacin rai ya juya yabar dakin.

Da dukuduku sukabi hanyar daji suna tafe suna waige Dan kar wani ya gansu sukaje bakin ruwan sai suka karasa inda ta boyeshi suna zuwa taganshi kwance yadda ta barshi ta hangoshi amma tana zuwa daf dashi taga wani katon miciji ya fasa Kai dai dai kansa da gudu ta karasa shikuma micijin ya feso dafinsa tay maza tasa hannunta ta tare tasaki wata razananniyar kara wadda gaba daya dajin yay amsa kuwwa ta Fadi a wajen.

Kubiyoni page na gaba yanzu labarin ya soma takuce.

Inagodiya ga masoyana masoyan wanna littafi inata ganin comment dinku nagaode sosai Allah yabar zuminci sainaji daga gareku.

*Feedyn bash*
[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: *?ARNAN DAJI?*

*?KAINUWA WRITERS??ASSOCIATION??*
{United we stand and succed;our ambition is to entartain & motivate the mind of readers}

FAREEDA ABDULLAHI

20-25

JINJINA AGAREKU

A matukar mamaki ta tsaya ya karaso kallane mahaifin rama inazaki a wannan daren ko suma zuwa zakuyi kutafi dasu a cinyesu kamar yadda kukaiwa hayaki bakuda adalci sai y fara hawaye jikinta yay matukar sanyi ba haka araina kalla nafika tsanar wannan abun saboda al adar garinku na rasa iyayena gwara kai dama kasaba al adarkuce nazo zan gana dasune bisa bikin daza ay na ja e da tenkwai bansan kowa yasan nafito katemaka karufa min asiri shikenan kije ina nan harki fito saboda bansan mezaki aikata musuba basu da kowa dan haka bazan bari ki cucesuba tasa kai gidan tana shiga ta hango haske a dakin da suka kai wannan majinyacin dasuka tsinto suna chan sun shagala wajen kulawa dashi saboda har yanzu beko motsaba suba sallama suke ba bare susan da zuwan mutum bama susantaba kai tsaye tafada dakin tana shiga tagansu gurfane gaban mutum suna samasa magani hankalinta a matukar tashe tace menake gani meye wannan kun boye mutum a gida kunsan ana neman mutum guda kunsan cewa wannan ba karamin lefi bane a razane suka jiyo jin magana abayansu hankalinsu be kara yashiba sai da suka juya sukaga mahaifiyar ja e ce nan lamunde tafara kuka kiyimana rai kitemaka mana badu yatemakeki tsintarsa mukayi a ruwa tausayi yasa muka kawoshi muka boye dan yasamu lafiya mu kaishi hanya ya gudu nan tenkwai ta matso ta kwashe duk irin wahalar dasuka sha ta sheda mata jikinta yay sanyi nakarbi uzurinku amma dole saina shiga cikin wnn lamarin saboda tsoron abunda zeje yadawo zanyi tunani akan maganar dama maganar auren tenkwai da ja e ta kawoni sarki ya bashi angama magana a fada a matukar razane tenkwai ta mike kimun rai kitemakamun banda kowa rayuwata ta lalace yazanyi kiyi shiru ki kwantar da hankalinki kinsan ba wanda ya isa ya hana wannan abu idan kukai gardama duk kasheku za ay kuma  kunsani kiyi hakuri ki aureshin abunda za ay idan anyi auren karki taba yarda dashi duk yadda za ay kafin musamu mafita karki bari yay miki komai tenkwai danane nasan bashi da kirki banasan sarautar garin nan ta kona hannunsa saboda ba wani sanji da za asamu dan ja e yafi kaho bakar zuciya wani abunma shiyake kara sawa ayi kullum fata nake sanji yazo nagode nagode badu ya temakeki zanyi yadda kikace bazan ketare umarninkiba zan miki biyayya zan auri ja e amma da sharadi gefenki za a ajiyeni karki damu tenkwai wannan me sauki ne shikuma wannan mutum zansan yadda za ay bari naje dare yayi nisa tajuya tafita tana fita ta tarar har yagaji yafara bacci kalla tashi nafito mutai karakani jiki a sanyaye ya mike yana danasanin abunda yay mata da fari

Sanda suka shiga kano biyar ta wuce afra tafara ajiyewa a gida sannan tawuce ta ajiye ummanta sai da safe umma zanyo miki aike tom shikenan diyar albarka taja motar ta tayi gida tana shiga ta tarar driver na sauke su asra da ansar daga makaranta tana ganin yaran zuciyarta takara baki kai musa driver tsaya na hadoma kayansu maza maza kamaidasu gidan su suhail nabarmusu gaba daya cike da mamaki ya tsaya yana kallonta tasa kai tana kwalawa maryama kira zoki hadawa su asra kayansu maza maza yanzun nan sai da takai bayan magariba tana hada kayan saboda yawansu saida ya fara kaisu dawasu kayan fal mota sannan yadawo ya kai ragowar asra ko ajikinta ansar nema yaketa kukan momy itako asara dama tafi sabawa da daddy kuma bayanan gwara ta koma gida hajiya kaka yafi mata sunfi bata kulawa hajiya ta kalli musa direba dayake shigo da kaya kai lafiya meyafaru hajiyace tace adawo dasu nan adawo dasu ba wani bayani ita metake yi wallahi bansaniba to allah ya kyauta kutaho nan yayan albarka allah ya bayyana mahaifinku duk halin dayake ciki kuyi hakuri ita kuma mahaifiyarku allah ya ganar da ita

Da sassafe rama ta shigo da kayan aikinsu na mahaifinta tace masa tenkwai ba lafiya zata dubata a galabaice tenkwai ta fito ta fada jikin rama rama na banu aurena ya tabbata waze kulamin da wannan mutumin dana tsinta ya shiga raina na fuskanci ba komai ke dawainiya daniba sai tsantsar soyayyar shi gaban rama ya fadi itama ahakan takasance tunda taganshi jiya ko bacci kasawa tayi tana tunanin wannan mutumin me hakan ke nufi sun fada soyayya da wanda basu san shiba ze mutu ko ze rayu basu da tabbas mutum ne kamarsu amma ba irin tufafinsu dayaba nashi ya rufe masa ko ina yanada kyau ba dan yankinsu bane yaza suyi nazarin da rama ta tafi kenan ki kwantar da hankalinki ki kaiwa badu kukanki ze temaka miki duk da shi yafisan sarki da ahalinsa amma ke ki jarraba cewar rama tana matsar hawayen itama duka biyu tana cikin tashin hanakalin rasa hayaki taga wannan jiya ya shiga ranta ashe tenkwai tarigata bata sake cewa komaiba ta shiga dakin ta baje kayansu na aiki tadinga mai masa wasu abubuwa kamar surkulle tana shaka masa wasu abubuwa tasa magani a ciwon kansa tasa kyalle tanade tanata zagayeshi dawani irin turare tanata wasu maganganu tamkar bokanya kawai sai ji sukai yanta wani irin tari me hade da atishawa a guje suka shiga dakin har suna yar rige rige tsakanin tenkwai da lamunde

Anan zan dakata sainaji ra ayoyinku nice taku akoda nake muku fatan alkhairi inajin dadin comment dinku gareni kwarin gwiywarku gareni da kaunar dakuka nunanwa rubutuna shiyake bani damar yi muku typing har so biyu a rana

*Feedyn bash*
[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: *?ARNAN DAJI?*

*?KAINUWA WRITERS?? association??*
{United we stand and succed;our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}

Gareku masoyana ina Mika godiyata gareku Allah yabar kauna naji Dadi yadda littafina ya karbu a wajenku wannan shine na farko Amma ina jin dadin yadda kuke bani karfin gwiywa nagode sosai??????????

FAREEDA ABDULLAHI

15-20

Umma meya kawoki wannan dajin mekikazoyi ya akay kikasan nan a tsorace ta kalleta tana kame kamen rashin gsky uhmm wlh dama um dama kawata hajiya asabece ta aikoni dama tana aikoki kenan saboda mugun hali bakya gayan cewar Jeddah to ame kikazo a motar haya nake me mashinne ya shigo dani iyaka temakamun Dan allah nataho sai mu koma kanon tare ki koma dawa wallahi baki isa kishigarmun motaba ki koma yadda kikazo matsalarki daban tawa daban Dan bakin ciki kinsan da nan din baki taba kawoniba sai aukin kice zakijemun gidan malamai mtsww haba jeddah mahaifiyarkicefa bekamataba gsky dolene mujirata tazo mutafi duk da itama lefintane data sanar miki daba saimuzo gaba dayaba mtswww wallahi taci darajarki afra wallahi da bazan jirataba ni da Allah ki sauri kizo mutafi to to Yar albarka bara nay sauri (kunjifa pans way Yar albarka uwa akewa wannan saboda ya tanaji da kudi Allah ya kyauta duk da itama uwar banzace Allah ya bamu iyaye nagari ameen)

A wahalce suka karasa gida sunyi sa a bawanda yagansu suna shiga cikin farin ciki tenkwai tace badu yatemakemu munzo lafiya ba Wanda yaganmu yauwa kisashi a wanchan dakin wanda ba a shigarsa anan zamu ajiyeshi zami taymasa magani har ya warke dan yana numfashi to lamunde nagode badu yasaka miki way ke meyasa kikesan wannan mutumin ganina dashi nafarko naji ya kwantamun araina nikaina wallahi lamunde bantabajin San wata halitta kamarsaba yanzu  b dai nibanajin Dadi sosai bangama dawowa dai dai ba kishiga daji ki hado magunguna na ciwon kan nasa da raunikan jikin nasa kafin ya farfado to tenkwai ki rufe dakin saboda kar wani ya shigo yaga anbude tana fita tenkwai ta koma dakin tazura masa ido ko kiftawa batayi Bata taba ganin mutum mekyansaba gashi ita tasan ba kyakykyawabace wannan yafi karfinta nesa ba kusa takura masa ido kawai sai ji tay an fado jikinta tay matukar firgita da razana tana dago Kai taga rama a jikinta tana wani irin kuka nan da nan takidime tajata sukabar dakin ta kulloshi kamar yadda lamunde tasata suka fito lafiyarki kuwa tenkwai inacikin masifa rayuwata tazo karshe badu bashi da imani ubangijinmune Amma Baya tausayamana kinsan saura wata biyu bikin shekara mutum daya ya rage Wanda za abawa badu jininsa anbada hayaki shiza ayanka Amma kaishi kurkukun ajiya nashiga tara tenkwai jib kamar kayan wanki tenkwai ta Fadi sai hawaye suka hadu suka dinga razgar kuka yanzu abunda sarki ya yanke kenan arasa Wanda za ayanka sai hayaki kodan anga iyayensa basu da karfi basu da komai a kullum inafatan karshen wannan mulki na zalunci yazo kiyi hakuri kinsan baza a taba fasawaba Dole shi zasu yanka kodako sun Sami wasu kiyi hakuri kawai nan sukayita kukansu harsuka gaji bayan tadan sami nutsu way ko tenkwai waye a cikin dakin chan Dana shiga naganshi akwance Nan tenkwai tafara kame kamen rashin gaskiya ki kwantar da hankalinki mu

Yan uwan junane sirrinki nawane waye shi Nan ta kwashe duk yadda akai tasanarwa da rama rama ta tausayamasa ki kwantar da hankalinki bame jin wannan maganar zantayaki kulawa dashi kinsan irin wannan aikin babanane Kuma Nima na lakanci duba marasa lafiya irin haka zan dubashi Amma sai hankalina ya kwanta bara naje gida zan komo gobe nadubashi narasa hayaki yazanyi da Raina takarasaka sabon kuka kiyi hakuri Nima ina cikin matsala ja e ya rantse wannan shekarar za a auramasani Kuma kinsan dole haka za ay banda wani zabi ta lallabata da kyar tarakata gida tadawo ta tarar lamunde ta dawo harta hada magunguna ta toshe masa kansa tasaka na sirace a wuta

Gaskiya Jeddah baki da mutunci uwarkicefa kike mata haka dallah kyaleta way tasanko abunda kika aikata hhhhhhh to ay ita tasani ita taban wannan shawarar Dan haka nibanda matsala da ita tana karasawa tazube gaisuwa nake boka me rangwangwen Kai kake da duna kake da gantali gafalalle uban gafalallu shege kake me maida shege yazamo tsinannne hhhhhhh barka da isowa yanzu yarki ta tafi ehhh munma hadu ita suna jirana zamu koma tare duna yatemakeka dama sonake akama mun ita a hannuna sai yadda nay da ita wannan dukiyar yazamana nizan dinga sata nizan hanata saboda boka batajin maganata hhhhhh tsinanniya ay za ay yadda kikeso Amma kisani zaday tadinga baki kamar bazasu kareba zata baki kamar me zubar da shara a bola haka zata maidake wajen baki kudi  Amma bazata taba yarda kidinga yadda kikaga dama da itaba zatayta baki kudi hhhhhh godiya nake boka ga wannan asiyawa jariran aljanu kayan wasa ke ya dakamata wata tsawa ba kudi nakesoba jikinki zaki ban kamar yadda kika saba jiki na rawa tace boka suna jirana kasan shedaniyar yarinyace kawartace tasa baki dama zasu jirani kasan wahalar danake sha wajen komawa hhhhhh ina ruwana Amma bazan bari su tafiba zan aika Dan digwi yanzu ya tsaidasu hhhhhh Nan d nan saiga wata bukka ta bayana ba tsoro ba komai tasa Kai ba abunda ke tashi sai wani masifaffen wari da karni yana wani irin hamami haka ya dosota tanaji tana gani tabashi kanta yay abunda zeyi da ita tsawon awa hudu yana abu daya haka ta fito a galabaice tana zuwa ta tadda su jeddah sunata nadar bacci ta sheke da dariya wani aikin sai boka ta tashesu sukaja motar suka dau hanyar kano tana gidan baya ta baje saboda tsabar gajiya ita kanta wani wari take

Badu yatemakeka ja e zegana dakai hhhhh kushigomun da gudan jinina yana zuwa ya zube kaho inaso ka auramun tenkwai a wannan shekarar inasonta itakadai koko dawasu a a ita kadai nakeso tukun angama gudan jinina ko matan garin nan duka kakeso za a aurama bare

tenkwai guda jallin jal angama kasa aranka tazama taka dama takace da farinciki ya fito daga fada burinsa ya cika an mallaka masa ja e yana zuwa ya samu mahaifiyarsa da maganar hankalinta ya tashi batasan ya lalata rayuwar yarinyar dantasan ainihin tarihinsu tasanta kwarai yarinyar kirkice tanajinta tamkar diyarta gashi sarki yabashi bame hanawa Dole ta dau mataki saida tabari sahu ya dauke ta sadada tafita   tadau hanya tanata sauri tazo dai dai gidan zatasa kafarta  jitay andaka mata tsawa ke inazaki a kidime taja ta tsaya

Shin waye ya dakawa mahaifiyar ja e tsawa kubiyoni a cigaban arnan daji Dan jin yadda zata kaya

*Feedyn bash*
[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: *?ARNAN DAJI?*

*? KAINUWA WRITERS?? ASSOCIATION??*
{United we stand and succed; our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}

FAREEDA ABDULLAHI

GAISUWA DA JINJINA AGAREKU MASOYANA INAJIN DADIN YADDA KUKE BIBIYAR

NOVEL DINA DA COMMENT DINKU DA KARFAFAMUN GWIYWA DAKUKE MUSAMMAN

KAINUWA WRITERS
ARNAN DAJI FANS
ZUMUNCI DANGIN JUNA GROUP
SADNAF FANS
KAINUWA FANS
MATAN SO GROUP
MATA MASU AJI GROUP

NASADAUKAR DA WANNAN PAGE DIN GA KANWAR MAHAIFIYATA AUNTY AYSHA INAFATAN ALLAH YAY MATA RAHMA DUK ME KAUNATA YAY ADDU A AGARETA ALLAH YA RAYA DIYAR DATA BARI ZUHURIYYA YAY MATA ALBARKA YA ALBARKACI RAYUWARTA

30-35

Agigice ya Mi'ke ya shiga saka wandonsa babu ko kunya tunda dama ba kunyar ce dashiba, gefe guda adu'kece kwance face-face cikin jini, daga chan waje d'aya a d'akin Kuma rama ce keta zunduma ihu mara sauti ta toshe bakinta.

Hankalin ja'e yay masifar tashi ganin tenkwai a sume, bawai aduke da take kwance ce itama rai a hannun Allah ba damuwarsa a'a shi masoyiyarsace damuwarsa, be so taganshiba duk da aurensu ba fashi.

Nan da nan ya fita ya debo ruwa ya zuba mata tasaki ajiyar zuciya tayi attishawa ta bude ido.

Tana ganinsa ta mi'ke a fusace ta sha'ki wuyansa da'kyar ya bambare hannunta daga wuyan nasa saboda ta fusata danma dama arnan daji 'karfafane ya zura da gudu harzata bishi ta fasa ta juya kan adu'ke tana jijjigata dakyar take numfashi ta sata agaba tama rasa me zatayi mata

"har gida dan iskanci" ta fad'a a zuciarta

jin shiru rama taleko d'akin taga tenkwai akanta da gudu tasa kanta ta rungumesu suka rungume juna rama ta fashe da kuka tace

"bake yazo nemaba aduke kin ceci tawa rayuwar kinbada taki ya wula'kantaki ya cuceki"

Aduke tasa hannu tarufe mata baki

"kiyi shiru rama mu aminan junane mu uku banda mahaifi banda mahaifiya banda kowa sai ku banajin zan cigaba da rayuwa" ta qarashe tana mai tsananta kuka

"kiyi ha'kuri baranazo nai miki magani"
"ki kyaleni karkimun komai indai d gaske kina kaunata" tenkwai takasa magana kawai ta rungumeta tana ajiyar zuciya kawarta aminiyarta tare suka taso su uku basa rabuwa amma rana daya Ana neman arabasu Kuma sunan Wanda za a aura mata baze yiwuba wallahi saita dau fansa bazata ta barin haka ta faruba duk da su a garinsu wannan ba bakon abu bane Amma sai kinyarda ita Kuma karfifa yasa ya farkata har haka kamar dabba sai itama ta kara fashewa da kuka da kyar aduke ta kamo hannunsu ta hada sannan tace
"kuyi hakuri kudena kuka" tana numfashi dakyar
" kusa wannan a matsayin kaddarata mu kawayene tun kuruciya kutuna da rayuwarmu ta kuruci mu masu rike amanane da sirrin juna karku sanarwa da kowa wannan zance Koda ko kakatace wadda nadauketa kamar uwata sirrine tsakaninmu Koda mutuwa nayi kumin alkawari"
Da sauri tenkwai tasa hannu ta rufe mata baki aduke takwantar d kanta akan cikinta ta cigaba da kuka
"garin Yaya haka tafaru wayay mata haka? " sukaji magana abayansu ana tambayarsu suka juya a tsorace dukansu jin maganar mutum.

Jeddah kwance tayi dai dai tanata aikata Masha'a dawani saurayi kwatsam Al ameen yasawo kansa falon bata taba tunanin wani ze shigo mataba Dan tasaba ba Wanda yake shigo mata sun Lula wata duniyar basu San ya shigoba sai ji sukayi yanata zabga salati a furgice ta juyo tana neman abunda zata sitirce jikinta dashi ya zuba musu ido kallon kun shiga uku yay musu Nan da nan ya cire belt dinsa yadinga jibgarsu sunata ihu bame ceto sai da yay musu jina jina yahada musu jini da majina Dan kansa ya gaji ya futa a fusace
Bangaren maryama ya nufa kai tsaye " nagode Miki kwarai maryama aikinki yana kyau duk abunda ake ciki kici gaba da gayamun Dan ubanta Dole ta bar gidannan zanje insamu hajiya akwai aikin dazami na tattara duk wasu muhimman takardun Yaya suhail d komai n bangaren dukiyarsa Kuma Dole ke zaki aikin"
"to yallabai nagode" tace masa
" karki damu fatana kuci gaba da zama yadda kuke karki taba nuna mata wani sanji nagode maki ay yanzu jikinta ya gaya mata" maryama murmushi kawai tayi.
Yana fita Jeddah ta dubi saurayinta tace "Ahmad ka cuceni Al ameen nake masifar so a yanzu shi zuciyata take bukata fiye da yayansa shine dalilin dayasa ban damu da batan yayansaba saboda dashi na shirya yin rayuwa yarone da kudi ga zubi me kyau ya tsaru ga kudi ga gayu

Kuma shi Dan fantamawane Amma tsinanne saida ka ribaceni saida nace muje daki ka kiya" yana tashi ya zabga mata mari ya kara mata da duka ta ko ina sannan yace " Dan uwarki lefin waye kina kallo ya hadamu ya jibga kuma yasanni yasan gidanmu kinsan meze biyo bayane kowa yasan kece kike nemana kekika jawoni tunda gidanki nazo tun kafin ki aure kike nemana kina bibiyata kowa yasani Dan haka kece a ciki kingama cin amanar mijinki Bata fa yay ba mutuwa b kike ikirarin auren kaninsa jaka kawai me kyan Dan miciji yasa kayansa harze fita Kuma sai y dawo bani kudi banda kudi bazan bayarba ko kobani Kona karairayaki ga rashin kunya ga Dan banzan tsoro itaba karfiba jiki a salube tawuce ta dakko masa rafar dubu dari ta wulla masa karbi kare ya fuce yabarta a wajen

Anan zandakata sainaji ra ayoyinku nagode sosai

*FEEDYN BASH*
[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: *?ARNAN DAJI?*

*?KAINUWA WRITERS?? ASSOCIATION??*
{United we stand and succed; our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}

FAREEDA ABDULLAHI

25-30

JINJINA AGAREKU MASOYANA MASOYAN WANNAN LITTAFIN NAWA ME SUNA ARNAN DAJI

Gaisuwa da jinjina agareku KAINUWA WRITERS ASSOCIATION Allah ubangiji ya karamana fasaha ya kara hada kawunanmu yabamu nasara akan wannan rubutu da muke Allah ya daukakamu

Aguje suka shiga dakin tabbas shine yake tari ruwa nata bulbulowa tabaki ta hanci harda Dan jini jini sukazo kansa suka durkusa rama tajuyo ta kalli tenkwai taga yadda farin ciki hade da tausayinsa ke kwaranya a idanuwan tenkwai sai jikinta y karayin sanyi tace kubashi iska bangamaba tukun da hanzari lamunde tasa Kai tafice dakyar tenkwai taja jiki ta fita tana tafe tana waiwayensa cike d tausayin kansu itada tenkwai rama tacigaba da aikinta na bokaye danko bokaye za akirasu tinda mesuka sani inbanda surkulle Allah yay mana tsari d jahilci tacigaba dayi masa surkullen sai data dauki minti arba in sannan tafito tahada gumi tagaji sosai ta kalli tenkwai da hanzari ta taso hartana zabga tuntube ya jikin nasa ya farkane tadanyi Jim kamar bazatace komaiba eh jiki da sauki yana numfashi yanzu ya farfado daga dogon suman dayay Amma yasamu bacci me nauyi ze iya kwana uku yana wannan baccin amma kullum zandinga zuwa ina dubashi inasa masa magani safe da dare zanje gida kizo inasan magana dake anjima tom rama nagode maki sosai badu yatemakeki ba komai tasa Kai tafuce

Abun duniya yadamu mahaifiyar ja e hari tunaninta Yaya zatay da wannan mutum data gani a gidansu tenkwai tabbas idan aka samu labari Koda wasa kaho yaji shine mutum na cikon biyar daza a yanka duk da ansa hayaki amadadin na biyar din tabbas akwai matsala amma tayaya zata temaki wannan kyakykyawan saurayi dole sai ta hanyar ja e to shima bakin mugune yamafi kaho mugunta tinda inka haifi da sai yazoma yafika Amma duk yadda za ay bazata taba bari asan dazaman wannan mutum ba Dole tasan abunyi saboda tabbas wannan bako ze musu amfani bata saniba ko shine silar gyaruwar wannan gari nasu tanajin hakan ajikinta a guje wata baiwa ta shigo badu yatemakeki ansamu haihuwar jarirai har mutum takwas wayanda akaiwa biki shekarar data wuce dukansu yanzu haka suna fada za ay bikin farfesunsu kwana uku masu

zuwa yakamata izuwa yanzu kisomacin naman jarirai Dan ba karamin Dadi gareshiba dakata shashasha tur daku dakuke iya cin naman yayanku da Yan uwanku kinsan zafi da radadin da iyayen wayannan jariran sukeji musamman ma mata su sukasan wahalar dasuke sha na haihuwa nasan yatake tabbas badu be cika abin bautaba Wanda ya haliccemu dukanmu Amma shize dinga shan jininmu tun tuni nasan akwai wani abun bautar bayan shi Amma namanta menene saboda Nima bamu da addini haka na taso amma anamu garin ba a haka tashi kiban waje jikinki har rawa yake kina murna xakici naman jarirai kema ba auren kikesoba a wannan shekarar zaki haihu zakiji zafin da sauran iyaye sukeji tashi kiban waje jiki asanyaye tabar dakin hari ta fashe da kukan tausayi tace munada bukatar sanji muna bukatar temako sai kuka

A a ansar kaidawa kukazo Ni da Yaya asra mamyn mu tadawo damu Nan gidan kamarya cewar al ameen kundawo nan ita kumafa metake nufi ya futa a fusace way hajiya me Jeddah take nufi ta turo miki yara iceko ita tana nata gidan uban Dan tunda bazata rike masa yayaba Dole tabar gidan dama darajar yayan akabarta a gidan ta koma nata gidan uban hajiya ta kalleshi meye naka natada jijiyar wuya badai gida bane taje tayta zama Ni hakanma yay mun Dadi dama da haka araina banasan Jeddah tarikesu saboda itama tarbiyya ba isarta tayba yay shiru zuciyarsa tanata tafasa ay shikenan Amma nasan abunda zanyi ya tashi ya fita itako Jeddah duniya sabuwa Nan ta bude shafin rashin mutunci tasallami duk masu aikin gidan maryama kawai tabari Dan itama taga batada sa idone Bata damu da itaba balle shiga bangarenta (datasan cewa meze biyo baya dabata bar maryamaba muje zuwa dai)hankalinta kwance tafara wadaka da dukiya Nan tanemi biza zuwa Dubai ta biya musu itada kawarta afra ummanta ko haka take tura mata da kudi hankalinsu ya kwanta basu da wata matsala bamesa musu ido tasayawa afra wata mahaukaciyar mota tasiya mata gida hankalinsu kwance aikin boka yayi tunda aka maidasu asra basu kara waiwayartaba dagasu har kakanninsu shiyasa takecin karenta ba babbaka anan tasamu hanyar zuwa manyan Park da gidajen shakatawa tafara haduwa da manyan alhazawa suka kara bude mata ido da kudi hankalinta kwance zata shigo gida da Wanda takeso suyi badalarsu San ransu tayi kawaye mata na garari matan manya tuni tafara janye jiki da afra matsalar daya tamusu biza tare d gsky bazatat tafi da itaba saboda idonta ya bude bame sata ko hanata kullum ummanta a cikin fasa mata Kai take kinganki kuwa lallai inada kadara kin hadu kinxama big madam lallai kudi sunyi yata tana fari tana iyayi Allah umma wallahi jeddah kullum aikinta kenan zuzutata ita Kuma taita mata barin kudi

Jiki a matukar sanyaye rama ta koma gida tabbas akwai aiki agabanta yaza tayi kenan ta rasa hayaki sai hawaye gashi a ranar data rasa shi takamu dasan wannan bakon dabatasan waye shiba Wanda ta tabbata ba irinsu bane yafi karfinta gashi shi duka jikinsa a rufe sabani su day komai gashi Nan a waje tasan tabbas aka kamasu hukuncin kisa yahau kansu dukansu sannan ga aminiyar ta itama tana masifar sansa to yazatayi da ranta tenkwai ko sai murna take Amma tana cike da alhini ance sai ya kwan uku ze farfado Amma duk da haka tana cikin farin ciki ta shiga ta tasashi agaba sai tadingajin wani sanyi a kirjinta tana ganin wannan mezatay da wannan mugun me mata Sama da ashirin ga kyakykyawan namiji itasam Bata jin zata yarda ay wannan auren to Amma yazatayi mahaifiyarsa ta roketa alfarmar tayarda ayi kodan tsira da rayuwarsu data wannan mutum tazauna tay shiru tana tunanin hanyar dazatabi tasamu mafita akan wannan mutum yamma nayi ta tafi gidansu rama tana shiga tajiyo nishi Sama Sama dawani irin gunjin kuka ta kara kaimi takarasa shiga dakin mezata gani wando tafara cin karo dashi ta kutsa kanta cikin dakin bemasan tashigoba tabbas shine shine  saidata rusa wani uban ihu tazube awajen ya juyo yaganta a matukar firgice ya Mike yana neman wandosa tabdijan.

Tofa muje zuwa metagani dayasata suma wa kuma tagani Wanda ganinta yasa shi firgita kubiyoni Dan jin yadda zata kasance nice ta ku harkullum

*Feedyn bash*
[9/11, 22:29] +234 810 679 5647: *?ARNAN DAJI?*

*?KAINUWA WRITERS?? ASSOCIATION??*
{United we stand and succed; our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}

BISSIMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DASUNAN ALLAH ME RAHMA ME JINKAI INAFATAN ALLAH UBANGIJI YABANI IKON RUBUTA LABARINNAN CIKIN AMINCI YARDA NA FARA LAFIYA ALLAH YASA NAKARE LAFIYA

FAREEDA ABDULLAHI

35-40

Jikinta gaba daya yay mata tsami wannan masifa hawan hawa yanzu duk yadda Ahmad yake mata biyayya haka ze mata yaro me masifar zaki gaskiya bazan iya rabuwa dashiba Nina janyo masa dukan dayacine yasa shi fushi kuma n tabbatar kunyace tahanashi rama mana wannan jibgar da mukaci zanbashi hakuri bayan nadawo daga Dubai Bari inkira waccen ta shirya muwuce tunda jibi zamu tashi gwara mufara shiri Amma Bata taba tunanin haka zata faruba saboda batasan zebata matsalaba Bata Kai sunansa wajen bokaba Amma bari tunda tafiya zatay saita dawo duk daya ganni da wani Dole ya aureni ay shima suhail b haka na kyaleshiba hanyar danabi nasami suhail ita zanbi nasameka Al ameen ko kaki ko kaso Nan tafara tunanin haduwarsu da yadda aurensu y kasance itada suhai shin wacecema Jeddah ne Bari muji

Jeddah kyakykyawace tagaske doguwa me matsakaicin jiki Bata cika faske bau ba Amma farace farinta me kyau daya hadu da shafe shafe tanada kyau ga gayu kawai matsalar talauci dayay mata katutu asalin iyayenta fulanin adamawane fatauci yakawo babanta malam jauro kano ya fara fataucinsa cikin nasara yana kawo shanu da awaki yana saidawa Allah yasa masa albarka yase gidansa medan kyau a dangwauro ya koma adamawa cike da farin ciki ya dakko iyalansa karkaso kaga daga hanci gun habi mijinta yayi gida zasu koma birni kano sunbar gidan gado kaf gidan tsoron habi suke saboda masifarta bame taba mata danta musammanma jeddah Yar gaban goshinta duka yayanta biyu kacal tahaifa a duniya sai Bari da taitayi daga Jeddah sai kaninta mansur mahaifiyarta macece jarababbiya mara godiyar Allah tun suna adamawa irin matan Nan ne masu bin malamai shiyasa ta mallake mijinta malam jauro bashida wani katabus sai abunda tasashi ganin Allah ya Bata ya me kyau data fara girma saita fara tunanin ita zata zame mata kadara( kunjifa fans ka haifi diya tazama kadara Allah ya kiyayemu)shiyasa tafara koya mata kissa da kisisina tuntana Yar sagaryarta tasaba zuwa shagunan maza suna latseta suna Bata kudi tana kaiwa uwarta kwanci tashi ba wuya taxama budurwa tasamu tagama secondary School dakyar daga Nan tafara yawonta na bin maza dama maza akwai San kyawawa to Jeddah tananfa Allah yay halitta kyaune da ita kamar aljana shiyasa take Jan zarenta San ranta shiyasa take kwasar samari tana hutawa da samari har makwadaiciyar uwartama ta samu abun da takeso ranta kal suci me kyau su sha me kyau suyi wadaka da kudinsu abun yanaywa malam jauro kuna yana cimasa tuwo a kwarya abun yana masifar Bata masa rai Amma anshanyeshi beda bakin magana baya iya cewa komai sai ido duk kokarin dayake akan iyalansa araine yake gun habi wannan rayuwa da yarsa keyi shine bakin cikin yasa masa hawan jini

Kwanci tashi ba wuya har sun shekara biyu da candy Jeddah tayi fice a kafatanin unguwarsu wajen tantiranci ga jarabar mahaifiyarsu malam jauro yayi yayi taida saurayi yay mata aure sunki itada uwarta gashi beda iko dasu ga mansur yazama tataccen Dan iska sai yay wata biyo bezo gidanba wannan bakin cikin shiyay sanadin da jininsa ya Kai dari biyu da hamsin sai da suka barshi ya galabaita sannan habi ta kaishi asibiti saboda su yayan basa Nan sun tafi gantalinsuAna zuwa asibiti kwanansa uku yace ga garin kunan yabar musu duniyar kowa yasha sha aninsa dama jeddah bata gidama kwananta tara saida ta dawo washegari habi mahaifiyarsu tanata rabzar kukan munafinci ta wayance kinga ikon Allah Ashe ko maganin baze shaba mutane suka zuba musu ido jin tana zance way magani bayan kowa yasan daga inda

jeddah take saboda mutunci da karamcin malam jauro maxajensu suka barsu suzo mata zaman makoki ba abunda ta bada Wanda za adafa na sadaka sai makota keta dawainiya Amma ba godi bare mun gode wata tace ina tajene taje karbo masa maganine a garinsu adamawa shiya turata Ashe ba rabon su gana itako matar ko shekaran jiya taga wuce warsu a mota adai dai Yan lemo sai Jeddah itama tafara kuka gsky duk iskancinta mutuwar mahaifi ba wasaba tayi kuka harta gaji sai bayan sadakar bakwai Nan Kuma suka balle ba uwa ba ya ko takaba habi Bata tsaya yiba mezataywa takaba ay ita Allah ne ya temaketa ya rabata da kaya yayinda dama mansur yazama fitaccen Dan iskane gagararre higher killers gashi Dan fashi kwace shaye shaye ba abunda bayayi na mugun abu nanfa duniya tabude musu sabuwa idon Jeddah ya kara budewa ta dada goge da bayan bariki akafara bin malamai kawai dai Bata shan komai

Tare sukai makaranta da afra secondary school tun suna makaranta basaji seat dinsu daya halinsu daya kawai ita dai afra ahannun matar uba take uwarta ta mutu shikuma mahaifinta bashida cikakkiyar lafiya baya fita ko ina yayyenta duk anmusu aure shiyasa lalacewar tata tay yawa b Koda suka gama makaranta kansu a hade yake sukaci gaba da tata duniyancinsu kowa yasan sirrin kowa Amma Jeddah tafi afra fitina suna yawonsu club club amma ita afra Bata kwana a waje karkarinta takai sha daya zuwa sha biyu na dare tana gida sbd tana shakkar babanta sosai dan idan tay dare sawa yake a Kira masa yayyenta suzo sunada mata na jaki to Kuma shi baya iya mikewa ba lafiya komai sai anmasa itake masa komai Dan ita matar tasa saitaga dama shiyasa takara samun damar yawonta bame samata ido Dan itama matar ubanta tanada kwadayi dataga tafara wanka zata fara lissafi asiyon kaza a tahon da kaza haka zatayta lissafi itako afra ko ajikinta tunda tasan tana rufa mata asiri babanta besan bin maza takeba yadauka kawai yawon gidan kawayene (kaji shashanci muje zuwa)

A razane suka juya wazasu gani baban rama ne da mado saurayin aduke Wanda za ay musu aure bana sunasan junansu so me tsanani anan mado ya durkushe yafara sharar kwalla duk dauriya irinta mazan ARNAN DAJI hakan besa ya daureba abun yay masa ciwo baban rama ya duka garin Yaya haka tafaru rama tafara kuka tafara magana muna zaune nida aduke mungacin farfesun kwadin datay mana mun ajiyewa tenkwai nata saita rigani wanko hannu bayan ta dawo saina fita Nima saina zaga bayan gida ina fitowa nadinga jin magana sama

